# KA SAN ABOKI NA?



Ina da aboki, masoyina. Ya fi kusa da ni.Ya na tare da ni kowane lokaci, kuma muna jin dadin tafiyar mu tare kwarai da gaske. Akwai abin da aboki na yayi mani wanda ba zan taba manta ba. An yanke mani hukunci mutuwa da kuma zuwa jahanama domin zunubaina, abokina yazo a maimaikona ya mutu. Yace idan dai na ba da gaskiya gareshi, bani kara zuwa jahanama kuma ba. Ni kuwa na yarda, na karbe shi, cikin zuciyata. Ya zo, ya ceceni daga zunubai na. Tun daga wannan lokaci yana cikin zuciya ta. Yanzu ina da salama da farin ciki kuma na sani wata rana zaya zo ya kai ni sama tare da shi har abada.

Ka san Aboki na yanzu? Sunansa Yesu Kristi ne. Ba domin na kadai ya mutu ba, amma har domin ka. Yana so ya zama Abokinka idan ka bada gaskiya gare shi, ka karbe shi cikin zuciyar ka, za ya zo ya taimake ka domin kar ka kara yin zunubi. Babu aboki mai kama da abokina!

Idan kana so Yesu ya zama abokinka, yanzu, kayi wannan addu'a, 'ya Yesu, ina so ka zama abokina na bada gaskiya ka mutu domin zunubaina. Ina furcin zunubaina da rokon ka, ka zo cikin zuciyata. Ka zarna Ubangiji na da Mai Cetona. Na gode domin karban addu'a ta, cikin sunan Yesu na yi addu'a. Amin!

Yabo ta tabata ga Allah! Yanzu, Yesu abokin ka ne, Tafi kada ka kara yin zunubi.

Idan ka yi kudiri domin Yesu ta wurin karatun wannan karamin kasida, sai ka rubuta mana domin mu yi murna tare da kai da kuma addu'a domin ka.